# Ya Allah ! Ina neman tsarinKa daga gajiyawa, da kasala, da tsoro da rowa, da tsufa, da azabar ƙabari, ya Allah Ka baiwa raina tsoranta, Ka tsarkaketa, Kai ne mafificin Mai tsarkaketa, Kai ne majiɓincin lamarinta kuma shugabanta, Ya Allah ina neman tsarinKa daga ilimin da ba shi da amfani, da zuciyar da bata risina, da zuciyar da ba ta ƙoshi, da addu'ar da ba'a amsarta

Daga Zaid Dan Arƙam - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Ba zan faɗa muku (komai ba) sai kamar yadda Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance yana faɗa: Ya kasance yana cewa: «Ya Allah ! Ina neman tsarinKa daga gajiyawa, da kasala, da tsoro da rowa, da tsufa, da azabar ƙabari, ya Allah Ka baiwa raina tsoranta, Ka tsarkaketa, Kai ne mafificin Mai tsarkaketa, Kai ne majiɓincin lamarinta kuma shugabanta, Ya Allah ina neman tsarinKa daga ilimin da ba shi da amfani, da zuciyar da bata risina, da zuciyar da ba ta ƙoshi, da addu'ar da ba'a amsarta ».
[صحيح] [رواه مسلم]

Ya kasance daga cikin addu'ar Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - «Ya Allah lallai ni ina neman tsarinKa» da fakewa gareKa, «Daga gajiyawa» rashin iko akan dabara mai amfani, «Da kasala» rashin samuwar niyyar yin aiki, gajiyayye ba ya iya yin wata dabara, mai kasala kuwa ba ta ma nufinta. «Da tsoro» ta hanyar hanuwa daga gabatowa akan abinda aikata shi yake kamata, «Da rowa» da hana abinda bada shi yake wajaba, «Da tsufa» yawan shekarun da zai kai zuwa ga raunin jiki, «Da azabar ƙabari» Da sabubban da suke kaiwa zuwa ga hakan. «Ya Allah Ka bawa raina» Ka bata kuma Ka datar da ita ga «Tsron Allahnta» da aikata ɗa'a da barin saɓo, «Ka tsarkaketa» Ka tsarkaketa daga ƙasƙanci da munanan ɗabi'u, «Kaine mafi alherin wanda Ya tsarkaketa» babu wani mai tsarkaketa inbaKai ba, «Kaine majiɓincinta» Mai taimakonta kuma mai tsaya mata, «Kuma shugabanta» Mai jiɓintar al'amuranta, kuma Ubangijinta Mamallakinta kuma Mai ni'imtar da ita. «Ya Allah lallai ni ina neman tsarinKa daga ilimin da ba shi da amfani», kamar ilimin taurari da bokanci da tsafi, ko wanda ba zai yi amfani a lahira ba, ko ilimin da ba za'a yi aiki da shi ba, «Da zuciyar da bata risinawa» gareKa, kuma bata ƙanƙar da kai, kuma bata nutsuwa, bata nutsuwa saboda ambatanKa, «Da ran da baya ƙoshi» ba ya wadatuwa da abinda Allah Ya ba shi kuma Ya azurta shi daga halal mai tsarki, «Da addu'a» abar juyarwa «wacce ba'a amsa mata».